**February 13th at 9:00 AM**
K Suites Hotel
No 21 Race Course Road
Nassarawa GRA,  Kano, Nigeria

**Girl Rising da tashar AREWA24 na sanar da fara nuna shirinsu na Da Bazar mu…**, wani sabon shiri da yake da kasha shida wanda zai zagaya da masu kallo sassanduni sannan ya sake dawo wa zuwa yankin arewacin Najeriya don shaida irin jajircewar da dan adam ke da ita da kuma tasirin da ilimi ke da shi wajen kawo sauyi duniya. Za a fara nuna shirin a tashar AREWA24 ranar 15 ga watan Fabrairun shekarar 2017 da misalin karfe 8:00 na yamma, haka kuma sabon shirin na rabin sa'a zai dinga zuwa a duk ranar talata cikin watan Maris.

*Da Bazar Mu…* yana bayyana abinda ya shafi ababen alfaharinmu kuma farin cikin mu : wato 'yayanmu mata. Kamar yadda muke fada da Hausa, 'idan ka ilimantar da 'ya mace, kamar ka ilimantar da al'umma ne ' shirin ya tattaro labaran wasu 'yan mata 12 da ba za'a manta da su ba da kuma himmarsu wajen neman ilimi- guda shida sun fito ne daga yankin arewacin Najeriya haka kuma guda shida sun fito daga sauran kasashe, wadanda suka hadar da kasar Ethiopia da Haiti da India da Nepal da Peru da kuma kasar Sierra Leone. Shirin zai dinga nuna matsalolin dake sanya 'ya 'ya mata ke fuskantar koma baya ta fuskar ilimi a arewacin Najeriya da ma duniya baki daya, da suka hada da auren wuri, rigingimu tsakanin jinsi da jinsi, bautar kananan yara, nuna banbanci tsakanin jinsi wanda yaki ci yaki cinyewa. A cikin kowanne labari, 'yan matan sun fuskanci manyan kalubale sun kuma tashi haikan don ganin sun cimma burinsu.

Tashar AREWA24 ce ta shirya shirin, wanda ya hada da wani abu daga cikin shirin fim na *Girl Rising*, da labaru daga yankin arewacin Najeriya wadanda aka gina su domin masu kallo wadanda ke magana da harshen Hausa. Kowanne shiri Hafsat Usman ta AREWA24 ce zata gabatar, kuma ya kunshi tattaunawa ta musamman da manyan mutane da masana da suka fito daga yankin arewacin Najeriya wadanda shahararren jarumin masana'antar shrya fina-finai ta Kannywood Ibrahim Muhammad Mandawari yayi. Sashen tattaunawar zai zaburar da masu kallo su kan su fara tattaunawa game da mahimmancin ilimin 'ya'ya mata a Najeriya. Za a bude layin waya na musamman don baiwa masu kallo damar kira da kuma samun shiga dan takai taccen binciken da ake yi da bayyana ra'ayoyinsu game da abinda ake tattaunaw a cikin shirin.

ShIrin *Da Bazar Mu…* ya hada da labarum da aka zabo  daga cikin fim din da ya sha suka wato "Girls Rising" wanda ya bunkasa ya zamo babban abinda ya yada sakon cewa ilimantar da 'ya'ya mata yana kawo cigaban al'umma. Milyoyin mutane a fadin duniya sun kalli Shrin Fim din Girls Rising, da yake taimakawa wajen sauya yadda mutane- kama daga iyaye zuwa shugabanni- ke kallo da kuma daraja gudunmawar da yara mata ke bayarwar ga al'ummar duniya, da daukar matakan tattaunawa a matakin unguwanni da kuma daukar matakan zaburarwa.

**QUOTES:**
A tattaunawa kan mahimmancin ilimin 'ya'ya mata da kuma tasirin shirin *Da Bazar Mu…* wajen kawo sauyi, Kwamishiniyar Harkokin mata ta jahar Kano, Hajiya Yardada Maikano, ta bayyana cewa **"na kalli shrin *Da Bazar Mu…* kasha daban daban, kuma naga yadda 'yan mata daba-daban da ke fukantar kalubale kuma suka shawo kan matsalolinsu. Ina jawo hankalin kowa da ya kalli wadannan labarai a matsayin wayar da kai game da matsalolin da yara mata ke fuskanta, da suka hadar da, Auran wuri da Auren dole da bautar da kananan yara da kuma banbanci tsakanin jinsi da sauransu."**

Game da hadin guiwarsu da Girl Rising, shugabar sashen shirye-shirye ta tashar AREWA24, Rakiya Usman, ta bayyana cewa **"matasan 'yan matan da suka fito a cikin wadannan labaru misalai ne na yadda ilimi zai iya budawa mutane damammaki da basu damar jan ragamar rayuwarsu da kuma bayar da gudunmawa ga cigaban al'umma baki daya."** Rakiya Usman, wadda ta rubuta kuma ta shirya shirin *Da Bazar Mu...* ta ci gaba da cewa, **"Dukkaninmu da muke aiki da tashar AREWA24 muna alfahari muga mun bada gudunmawa ga cigaban duniya ta hanyar amfani da ilimi a matsayin wani makami da zai bawa matasa dama kaiwa ga wata rayuwa da zasu kasance cikin abubuwan da suke mafarkin kasancewa."**

**Don kara sanin wani abu game da shirin Da Bazar Mu... sai ku ziyarce mu @ www.girlrisingnigeria.org**

Press Contacts:
Maryam Tafida
+243 08033612001

**Game da Girl Rising:**
Girls Rising shirin wayar da kai ne na duniya akan ilimin 'ya'ya mata da kuma koya sana'o'i. Girls Rising na amfani da tasirin bayar da labaru-ta hanyar shirya fina-finai, Radio da sauran kafafen yada labarai- don sauya irin tunanin da mutane ke yi akan 'ya'ya mata da daraja su. Tare da hadin guiwar abokan hulda na gida, Girl Rising ya kaddamar da gangami don kawo hanyar duba kan abubuwan da yara mata ke fukanta, samar da tattaunawa da kuma zaburar da mutane su shawo kan matsalolin dake kawo musu koma baya. Gwamnati da kungiyoyi masu zaman kansu da hukumomi da makarantu na amfani da aikinmu don auna tasirinsu da kuma kawo sauyi ga rayuwar 'ya'ya mata. Girl Rising a yanzu haka tana aiki a kasar Indiya da Najeriya, Jamuhuriyar Dimokradiyyar Congo da kuma Amurka.

**Game da AREWA24:**
Tashar AREWA24 tasha ce ta farko a kasar nan kuma it ace kadai tashar dake shiryawa da kuma yada shirye-shiryenta cikin harshen hausa sa'o'I 24 kyauta. Kuma wadda aka sadaukar da ita ga tsarin rayuwar da Al'adu da Matasa da Wasanni da wasannin kwaikwayo da fasahar zane da kuma nishadantar da iyali na Arwacin Najeriya. Mayar da hankalin da Tashar AREWA24 ta yi wajen bunksa shirin talabijin da Harshen Hausa, ya cike gibin da masu Magana da harshen hausa ke fuskanta a fadin duniya, wadanda da yawansu ke dawowa kallon Tashar AREWA24 ta hanyar amfani da manhajar yanar gizo a matsayin wata hanya da zata sada su da al'adunsu daa kuma al'ummun duniya. Ana saka Shirye-shiryen Tashar AREWA24 a kowanne mako aka shafin youtube.com/AREWA24channel, tashar tana samun matukar karuwa ta hanyar tattaunawa da masu kallonta a shafukanta na sada zumunta AREWA24.com, facebook.com/AREWA24,Instagram.com/AREWA24channel, da kuma twitter.com/AREWA24channel. AREWA24 zaku iya kama tashar a DStv (Channel #261) da GOtv (Channel #101) haka kuma akan EUTELSAT 16A, horizontal polarization, frequency 10804, symbol rate 30000. Abokan huldar AREWA24's wajen yada shry-shiryenta sun hada da Multichoice-Nigeria, da Eutelsat da kuma Jordan Media City.

**Domin Karin bayani sai a tuntubemu a kan: info@arewa24.com**